**EPISODE 21**

**<u>Characters</u>**

*Inna*

*Laraba*

*Alhaji Bature*

*Mai-Ungwa*

*Hassan*

---

**Scene 1**

**Northern Kaduna, Hajiya Inna's house.**

1. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**
2. **SFX:** **<u>SOUND OF FOOTSTEPS AS LARABA ENTERS INNA'S ROOM.</u>**
3. **LARABA:** *Assalamu alaikum* Hajiya Inna. Barka da rana, yaya jiki?
4. **INNA:** *Amin Wa' Laikum Salam* Laraba. Kin dawo? Barkan ki da dawowa. Yaya aikin?
5. **LARABA:** E, na dawo Inna. Aiki alhamdillah, ina fatan kina samun karfi yanzu ?
6. **INNA:** E na dan ji karfi kwarai. Laraba Allah saka miki da alheri, kullum kina cikin duba ni, ina jin dadin hakan. Tun da kika tare gidan na nake samun sauki kullum,. *Alhamdulillah!*
7. **LARABA:** **(SMILING)** *Haba* Inna, Ba wani abin da sai kin gode min bane ai, ai baza a hada da abinda ki ka yi min ba.
8. **INNA:** Menene nayi? Ni ban san wani abin da na taba yi miki ba fa Laraba, sai dai abin kyautatawan da kike yimin harma da yaya na. ba kit aba nuna mana bacin rai ba duk da suna bata miki rai.
9. **LARABA:** Inna, kin bani gida kuma kin dauke ni tamkar yar cikin ki, ai wannan ma kadai ya isa inyi godiya, nagode.

| | | |
|---|---|---|
| *10.* | **INNA:** | Oh wannan ne? kada ki dame kanki mamata. Ai na dauke ki kamar yata saboda kin chanchanta. Kuma ina fatan idan 'ya'ya na su tsici kansu a wane garin suma za su muri hakan. |
| *11.* | **LARABA:** | Na gode inna. Bari in shiga ciki in huta, yau na gaji |
| *12.* | **INNA:** | **(CALMLY)** Laraba. Dan jira don Allah, na lura cewa akwai abinda ke damun ki. Menene? Hankalin ki a tashe? |
| *13.* | **LARABA:** | Inna ina lafiya, ba wani abu, gajiya ne kawai. |
| 14. | **INNA:** | **(CONCERNED)** kin san yanzu kina matsayin yata ai nasan lokacin da kike cikin damuwa, kin rame kuma baki jin dadi. |
| 15. | **LARABA:** | **(SMILING)** Lafiya lau Inna, kilar gajiyar aiki ne kawai ke damunna. |
| 16. | **INNA:** | Laraba, bana jin dadin yadda nake ganin ki haka. Ban yarda cewan komai lafiya ba, ai komai neni kina iya tattauna da ne. |
| 17. | **LARABA:** | Na gode Inna. Idan akwai wata matsalla tabbas ki zan fara gaya wa ai. |
| 18. | **INNA:** | Toh, tunda kin dage. Yauwa kin tuno min ma, ina wacen saurayin Dacta? Nayi kwana biyu ban gan shi a gidan na ba. Ina fatan lafiya? |
| 19. | **LARABA:** | Yana lafiya. Muna dan samun matsalla acikin yan kwanakin nan. Kuma bana jin za mu iya warware matsalolin. |
| 20. | **INNA:** | **(SYMPATHETIC)** Eyyah! Kiyi a hankali fa ko kuma kid au hutu ki tafi gida, iyayen ki su dan kula dake. Kina bukatar hakan musammam ma cikin wannan yanayin naki da ki k ace lafiya. |
| 21. | **LARABA:** | Inna iyaye na sun rasu. |
| 22. | **INNA:** | **(SYMPATHETIC)** *Inna lillahi wa inna ilaihir raji'un!* mutun baya wuce ranar sa, sai hakuri. *Allah ji kan su.* |
| 23. | **LARABA:** | *Amin* inna nagode. ba komai Inna ai har ya zama jiki ma. |
| 24. | **INNA:** | **(PROMISING)** Kada ki damu Laraba, daga yau kin zama tamkar yata, kinji? |
| 25. | **MUSIC:** | **<u>BRIDGE MUSIC</u>** |

**Scene 2**

**Northern Kaduna. Mai-Unguwa's House. Evening.**

| | | |
|---|---|---|
| 26. | **SFX:** | <u>**SOUND OF MOVING MOTORCYCLES FROM THE DISTANCE. RANDOM AMBIENCE.**</u> |
| 27. | **MAI-UNGUWA:** | Alhaji Bature, ina ta tambayan menene ya faru tsakanin ka da matar ka tun dazu, amma baka cewa komai. |
| 28. | **ALHAJI:** | **(CHUCKLES BITTERLY)** Hmm Mai-Unguwa, Me kake son in fada maka ne? |
| *29.* | **MAI-UNGUWA:** | Abinda nake son in sani shine dalilin da tasa kake zargin Hindatu, matar ka ta farko mazinaciya. Wannan zargin babbar abune fa kuma ka san hakan. |
| 30. | **ALHAJI:** | Na san hakan. Kuma ba sharri nayi ma taba. |
| 31. | **MAI-UNGUWA:** | Mmhmm, Alhaji Bature ka kula da abinda kake fada fa, kasan baza a dauke maganan nan da was aba. |
| 32. | **ALHAJI:** | E nasa ni. |
| 33. | **MAI-UNGUWA:** | Kuma ka dai san akwai babbar hukunchin zaton wani da aikata zina, ko? |
| 34. | **ALHAJI:** | Mai-Unguwa nasan duk wadan nan. Kamar inda na fada maka, ba zargin ta nake yi ba. Ina da hujar cewa ya'ya' wajen Hindatu ba yara na bane. |
| 35. | **MAI-UNGUWA:** | wayyo Allah! Me kake fada ne Alhaji Bature? Wace irin hujja che kake dashi da baka taba ambatta ba duk tsawon shekarun baya sai yanzu? |
| 36. | **ALHAJI:** | **(CLEARS THROAT)** Naje asibiti nag a likita, anyi min gwaje sakamakon ta nuna cewa bani da isheshen karfin bay a mace ciki. Shine ma dalilin da ban samu haihuwa ba duk tsawon shekarun nan. |
| 37. | **MAI-UNGUWA:** | **(SHOCKED)** Me kace?! Ka tabbata? Abin mamaki! |

38. **ALHAJI:** Na tabbata mana. Yanzu ka dei ji hujja ta, nacewar ya'ya' wajen Hindatu ba yara na bane. Kuma ban kira ta mazinaciya ba, ni dai abinda nake cewa shine ta maida su wajen mahaifin su kawai.

39. **MAI-UNGUWA:** ni har yanzu ban gansu da hujjar nan taka ba, nasan dai akwai bukatan Karin bayani saboda Hindatu macece kamila..

40. **ALHAJI:** kana ji Mai Unguwa, ni abinda nake bukata da Hindatu shine ta fada min ainihin mahaifin yaran.

41. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**Scene 3**

**Northern Kaduna. Hajiya Inna's House. Evening.**

42. **SFX:** **<u>SOUND OF COMPOUND AMBIENCE. SOUND OF APPROACHING FOOTSTEPS.</u>**

43. **HASSAN:** *Assalamu Alaikum.*

44. **INNA:** *Amin Wa' laikumum Salam.*

45. **HASSAN:** *Sannu Inna. Ina yini? Ya jikin ki?*

46. **INNA:** *Yauwa sannu Hassan. Lafiya lau, kuma jiki da sauki.*

47. **SFX:** **<u>SOUND OF FOOTSTEPS AS HASSAN MAKES TO ENTER HIS ROOM</u>**

48. **INNA:** Hassan kada ka karasa ciki tunkuna, ina bukatar ganin ka.

49. **HASSAN:** Toh Inna, gani. Ina fatan dai lafiya?

50. **INNA:** E lafiya lau da'na. zauna

51. **SFX:** **<u>SOUND OF SMALL LOCAL CHAIR BEING PULLED AS HASSAN SITS</u>.**

52. **HASSAN:** Na'am mama, menene?

53. **INNA**: Hassan, menene ke faruwa tsakanin ka da twagyayen ka Husseini?

54. **HASSAN:** Inna, Hussaini yana son in janye takarata, saboda maigidansa Alhaji Bature na da nashi dan takara, kuma suna ganin nine zan iya ja musu cikas. Ki kuma tuna fa shi Hussaini yazo yadage in shiga siyasa.

55. **INNA:** **(SIGHS HEAVILY)** Hmmm, Hassan. Shike nan?

56. **HASSAN:** Na'am shikenan fa Inna.

57. **INNA:** (**CONCERNED**) Hassan, bana jin dadin yadda abin nan ke faruwa haka. Yaya za'ace yan'uwa kamar ku, tagwaye ma, wai kuna samun sabani akan abu kamar haka. Ba abin kunya bane a gare ku?

58. **HASSAN:** Inna ba laifina bane fa, idan ma ace shi Hussaini ne ke son matsayin, wallahi zan janye ba tare da wata matsala ba. Amma wani na chan daban. Ba ma Alhaji Bature ne ki son matsayin bafa, a'a dan takara shi ne wai *Haba! Yaushe. Gaskiya ba zai yiwu ba.*

59. **INNA:** Amma abinda yakamata kasani shine, duk abinda Alhaji ke so tamkar Hussaini ne ke son abun. Kada ka mance mai gidansa ne fa, kuma ya taimaka wa dan'uwan kwarai .

60. **HASSAN:** **(DISAGREES)** A'a Inna. Hussaini bai dauko abubuwan daidai ba, shi ya soma kuma yanzu yana son sulhu. Sam, bazai yiba, tunda ya gwamace Alhaji fiye da ni, ai sai mu zuba mu gani.

61. **INNA:** Hassan, ka ga inda kake yin kuskure ko, ba yadda Hussaini bazai taba gwamantar Alhaji fiye da kai ba, ai yasan kai dan'uwan sa ne, kuma yana kaunar ka kwarai .

62. **HASSAN:** Toh Mama, ai ba hakan yake nuna wa ba.

63. **INNA:** Hassan, ka gane cewa tsoron Hussaini shine kada Alhaji ya daina taimaka masa, hakan kuma tasa ya dawo gidan jiya, ai sai yasa yake neman wannan alfarman .

64. **HASSAN:** Inna, ki ajiye alfarma a gefe. Kafin yasan Alhaji ai yana yi wani abu, kuma yana rayuwa.

65. **INNA:** Hakika! Allah na taimakon mu kullun.

66. **HASSAN:** Toh idan Alhaji yak i yi masa alfarma, ai bazai mutu ba, tunda ya gwamamce alfarma akan dan'uwan san a jinni, nina na gwamace takarar ko da wanene. Kawai!

67. **INNA:** **(PLEADING)** *Haba* Hassan! Kaine babba fa. Ka kwatatta hakan kayi baza da duk wawacen da kaninka yayi. Ni abinda nake so shine ku sansanta da dan'uwanka.

68. **HASSAN:** Inna, menen hussaini ke son inyi? Sansantawa shine ya kyale ni in yi takara ta, ba ruwansa, kamar yadda na soma. Kawai!

69. **INNA:** A'a, ka dau girma ka janye takarar. Suyi dukan abinda suke son suyi yanzu. Nan gaba sai kayi takara a karni mai zuwa. Na tabbata zaka same dama.

70. **HASSAN:** Haba Inna! Me ya sa za kice hakan?.

71. **INNA:** **(PLEADING)** Hassan, don Allah ka kyale. Ko saboda lafiyata. Duk irin wadanana abubuwan su ke sa jinni na ke hawa fa, idan wani abu ya faru da ni, ku zai dawowa.

72. **HASSAN:** Inna, insha Allah ba abinda zai same ki. Kada ki mance cewa Laraba na kula da ke kullum.

73. **INNA:** **(PLEADING, CLOSE TO TEARS)** Hassan dana, don Allah ka sasanta da dan'uwan ka ko saboda ni, ehn?

74. **MUSIC:** <u>**BRIDGE MUSIC**</u>

**Scene 4**

**Northern Kaduna. Alhaji Bature's shop. Late Afternoon.**

75. **SFX:** <u>**SOUND OF ROAD AMBIENCE. RANDOM VOICES IN THE BACKGROUND.**</u>

76. **LARABA:** *Assalamu alaikum* Alhaji Bature. Yaya kasuwar?

77. **ALH. BATURE:** *Amin Wa' alaikum Salam* Laraba. Ah! Mun gode Allah, komai na tafiya daidai.

78. **LARABA:** Toh Alhamdillahi, Alhaji ina son inyi sayyaya.

*79.* **ALH. BATURE:** **(SMILING)** Toh, bisimbillah, dauke duk abinda kike bukata.

*80.* **LARABA:** **(SMILING)** toh,nagode. Erhm, Alhaji muna godiya kwarai da taimakon da kake yi ma kungiyan lafiyar nan ta al'uma, abin na mutukar rage mana matsaloli.

*81.* **SFX:** <u>**SOUND OF A NYLON BAG RUSTTLING**</u>**.**

*82.* **ALHAJI:** *Haba* Laraba! Ai ba wani abu neba. Bayan ma abun dukan al'umar ne.

| | | |
|---|---|---|
| *83.* | **LARABA:** | ba ma haka ba, tun da aka soma kungiyar asibitin ma ki cin gaba. Kungiyar nada fa'ida kwarai. |
| *84.* | **ALH. BATURE:** | gaskiyan ki |
| *85.* | **LARABA:** | kar ka so ka gani yawan mutanin da ki zuwa asibiti don nema sani da Karin bayani akan hanyoyin tazarar haihuwa. |
| 86. | **ALH. BATURE:** | **(IMPRESSED)** Ah hakan yayi kyau |
| 87. | **LARABA:** | **(HAPPILY)** Kasan muyi tayin muhara akan hanyoyin tazarar haihuwa wa jama'a, yasa abin tazo da sauki wajen tattauna hanyoyin a tsakanin maaurata. |
| 88. | **ALH. BATURE:** | **(HAPPILY)** Yayi kyau sosai, nayi farin cikin jin hakan. Mun yi saar samun nars mai kwazo da rikon aiki kamar kea nan al'umar tamu, ai ke baiwa ce gare mu. |
| 89. | **LARABA:** | **(THANKFUL)** Alhaji na gode. Yauwa, ina labarin abokinka? Ya samu ya ga likitar kuwa, akan maganar da muka yi da kai? |
| 90. | **ALH. BATURE:** | **(SMILING, ALMOST WHISPERING)** Laraba kenan! Ai ba wani ki fama da damuwan chan ba. Nine. |
| 91. | **LARABA:** | **(SURPRISED)** Alhaji Bature! Kaine? Toh meyasa baka fada min cewa kaine ba? |
| 92. | **ALH. BATURE:** | **(CLEARS THROAT)** Oho fa. Na rasa inda zan fito miki da maganar ne. amma naga Dacta Daoud . |
| 93. | **LARABA:** | **(EAGER)** Yayi kyau, me y ace? |
| 94. | **ALH. BATURE:** | **(SADLY)** sakamakon gwajin ba dadi samsam. Yace sakamakon ta nuna cewa zaiyi wuya in ba mace ciki. Amma ina da ya'ya' uku. |
| 95. | **LARABA:** | Toh!  Ina ma da wani sakamakon ba wannan ba. |
| 96. | **ALH. BATURE:** | Abin takaice, ba wani sakamakon. Abinda da ke ban haushi shine yadda matata na farko ta ci amanana. |
| 97. | **LARABA:** | A'a Alhaji kada k ace haka tukun na. |
| 98. | **ALH. BATURE:** | Amma sakamakon ta riga ta nuna ai, ba wani abun yi ai Laraba. |
| 99. | **LARABA:** | Alhaji akwai. Akwai abinda ake kira rashin kara daga baya, wato hakan zai iya faruwa bayan ka haiyayafa. |

100.**ALH. BATURE:** **(UPSET)** E amma Laraba, in azan same kwanchan hankali. Menene zai tabbatar min cewa nine uban wadan chan yaran .

101.**LARABA:** Alhaji kana iya yin gwaji domin ka tabbatar cewa yaran kane. Hakan zaka iya sanin ko ya'yan' kane ko ban aka ba.

102.**ALH. BATURE:** Amma Laraba, akwai yiwar cewa ya'ya' na ne? kodai matata ta farko ta dauke ne sakare duk tsawon wadan nan shekarun?

103.**LARABA:** Kamar yadda nace, kada ka yanke hukunchi tukun na, idan kayi haka ba kyautawa bane ma Hajiya Hindatu. Ka daiyi wannan gwajin da na fada maka

104.**ALH. BATURE:** Nars Laraba, kin ce gwanjin sani ko yara na ne, eh? Shawarar nan tayi. Ina dai fatan kada wannan gwajin ya tabbatar mini da abin da nake zargi.

105.**MUSIC:** <u>**THEME MUSIC**</u>